(١)

## YANAYIN YAYE DAMUWA DA TSANANI

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Ka ambaci lokacin da Ubangijinka ya yi shelar cewa: lallai idan kuka gode mini zan ƙara maku..)** [Ibrahim: 7]. Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

A cikin sunnonin Allah Maɗaukakin Sarki cikin halittarsa ne, ya sanya rayuwa ta zama tana kewayawa ne tsakanin tsanani, da yaye damuwa, da ƙunci da yalwa, da tsakanin baƙin ciki da farin ciki, masu imani ne suke zama cikin yanayi haƙuri da godiya a dukan waɗannan halayen, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Ina mamakin al'amarin mumini, lallai gaba ɗayan al'amurransa alhairi ne -babu wanda yake da irin wannan banda mumini- idan abin farin ciki ya same shi ya gode, hakan kuma ya zama masa alhairi, idan kuma cutuwa ce ta same shi sai ya yi haƙuri, kuma hakan ya zama shi ne alhairi a gare shi).**

Lallai cikin abubuwa masu kyau da suke ƙawata ayyukan Allah mai girma da ɗaukaka, yakan kawo yaye damuwa bayan an shiga cikin yanayi na tsanani, ya kuma kawo sauƙi bayan wahala, Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Lallai akwai sauƙi tare da kowace wahala, tabbas akwai sauƙi tare da kowace wahala)** [al- Sharhi: 5- 6], idan al'amari ya ƙuntata sai kuma ya yi yalwa, babu yanda

za a yi tsanani ɗaya ya rinjayi sauƙi biyu, bayan tsanani, babu wani abu da ya wuce yaye damuwa, bayan wahala, babu komai da ya wuce sauƙi da jin daɗi, Annabinmu ( SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai akwai yaye damuwa a tare da kowane baƙin ciki, kuma lallai akwai sauƙi a tare da kowane tsanani da wahala).**

Duk wanda ya dubi rayuwar Annabawa (Alaihimus Salam) zai ga wannan ma'anar ƙarara, ga Sayyiduna Ya'aƙub (AlaiHis Salam) nan da ya rasa wanda ya fi so a cikin 'ya'yansa, wato Annabi Yusuf (AlaiHis Salam), sannan bayan wasu 'yan shekaru kuma ya sake rasa ɗansa na biyu, har dai ta kai ga ya rasa idonsa saboda tsananin kuka da damuwa da rabuwa da ya yi da 'ya'yansa maza biyu: **(Har idanuwasa suka yi fari saboda da baƙin ciki yana cikin damuwa)** [Yusuf: 84], amma duk da haka bai ɗebe ƙauna ba, kaman yanda Alƙur'ani mai girma ya kawo a bakinsa cewa: **(Ya ku 'ya'yana, ku je ku binciko mini Yusuf da ɗan uwansa, kada ku ɗebe ƙauna daga rahamar Allah; saboda babu masu ɗebe ƙauna daga rahamar Allah sai jama'an da suka kafirce wa Allah)** [Yusuf: 87], sai kuwa ga yaye damuwa ya zo masa daga Allah mai girma da buwaya, bayan wannan tsanani da bala'i, Allah ya dawo masa da idanuwansa da 'ya'yansa, Allah mai girma yana cewa: **(Lokacin da albishir ya zo masa aka jefa masa a fuskarsa, sai idanuwansa suka dawo, sai ya ce: Ashe da ma ba na faɗa maku cewa na san wani abu a wurin Allah da ku ba ku sani ba?!)** [Yusuf: 96].

Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya tseratar da Annabinsa Yunus (AlaiHis Salam) daga duhun kogi da na dare da na cikin kifi, sai ya sauya masa damuwarsa ta koma sauƙi, ya sauya masa ƙunci ya koma yalwa da yayewa, Allah Maɗaukakin Sarki yana

cewa: **(Shi ma Zannun lokacin da ya fusata ya tafi abinsa, ya zaci ba za mu iya yin iko da shi ba, sai ya ɗaga murya ya yana cikin duhunnai uku yana roƙon cewa: Lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai kai, na ambaci tsarkinka ya Ubangiji, lallai ina cikin waɗanda suka zalunci kawunansu. Sai kuwa muka amsa masa muka tseratar da shi daga baƙin ciki, da ma kaman haka muke tseratar da muminai)** [al- Anbiya'i: 87]

Allah Maɗaukakin Sarki ya azurta Sayyiduna Zakariyya (AlaiHis Salam) da ɗa, bayan shekarunsa sun ja, ƙashinsa ya yi rauni, namansa ya zagwanye, furfura kuma ta mamaye kansa, Allah ya amsa addu'arsa a lokacin da ya roƙa ya ce: **(Ya Ubangiji ka ba ni zuriya mai tsarki daga wurinka, lallai kai mai yawan amsar addu'a ne. Sai kuwa Mala'iku suka kira shi yana tsaye yana sallah a mihrabin sallah, cewa lallai Allah yana yi maka albishir da ɗa sunansa Yahya, yana gasgata saƙon Allah, kuma shugaba ne shi kuma kamamme, kuma Annabi ne daga cikin salihan bayi)** [Ali Imran: 38- 39].

Lallai duk wanda yake yi wa nassoshin Shari'ar Musulunci kallo na tsanaki, zai ga inda Allah mai girma da buwaya ya samar da ƙofofi da mabuɗai masu yawa na yaye damuwa, a cikin su akwai: lizimtar tsoron Allah, da komawa zuwa ga Allah mai girma da ɗaukaka ta hanyar yawaita addu'a, da ambaton Allah da zikiri, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Duk wanda ya dogara ga Allah, to lallai Allah zai samar masa da mafita. Zai kuma azurta shi ta duk inda ba ya tsammani, duk wanda ya dogara da Allah, to lallai Allah ya isar masa, lallai Allah mai cika al'amarinsa ne, ya kuma riga ya sanya wa komai iyaka)** [al- Ɗalaƙ: 2- 3], haka ma Mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Shin wane ne yake amsa wa wanda ya shiga cikin damuwa**

**addu'arsa, ya yaye masa damuwa, ya kuma sanya ku zama ku ne kuka gaje doron ƙasa?! Shin akwai wani Ubangiji ne tare da Allah?! Ba za ku yi tunani ba ne?!)** [al- Namli: 62], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yakan yi addu'a da waɗannan kalmomin a lokacin damuwa yakan ce:

**لا إله إلا الله العظيم الحليم، لا إله إلا الله رب العرش العظيم، لا إله إلا الله رب السماوات ورب الأرض ورب العرش الكريم،**

Haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda damuwa, ko baƙin ciki, ko rashin lafiya, ko tsanani ya same shi ya ce:**

**الله ربي لا شريك له**

**Za a yaye masa)**.

***

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga cikamakin Annabawa da Manzanni, shugabanmu Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Wane abu ne ya fi kyau sama da mutum ya dawwama wajen ambaton Allah Maɗaukakin Sarki a duka halayen tsanani da na yaye damuwa, da halayen bala'i da na samun sauƙi, kada ya zama cikin waɗanda Alƙur'ani mai girma ya gargaɗe mu game da ayyukansu, inda suka manta da ambaton Allah a lokacin sauƙi da jin daɗi, ba sa gode wa ni'imominsa, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa a lokacin da yake yi mana gargaɗi game da ayyukansu: **(Idan wata cuta ta sami mutum sai ya roƙi Ubangijinsa, yana mai komawa zuwa gare shi, sannan idan ya**

**ba shi wata ni'ima daga gare shi sai ya manta abin da yake roƙonsa kafin wannan lokacin, ya sanya wa Allah kini da kishiya; saboda kawai ya ɓatar da mutane ga barin hanyar Allah..)** [az- Zumar: 8], haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Idan wata cuta ta sami mutane sai su roƙi Ubangijinsu suna masu komawa zuwa gare shi, sannan idan ya ɗanɗana masu wata rahama daga gare shi, sai ka ga wasu daga cikinsu suna haɗa Ubangijinsu da wani a wajen bauta)** [ar- Ruum: 33], haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Idan wata cuta ta same ku a lokacin da kuke cikin kogi duk abubuwan da kuke bauta wa waɗanda ba shi ba ɓace maku suke yi, sai shi kaɗai kuke roƙa, idan kuma ya tseratar da ku ya kai ku gaɓa, sai ku juya masa baya, lallai ɗan Adam ya kasance mai yawan butulci ne)** [al- Isra'i: 67], haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Idan wata cutuwa ta sami mutum a rayuwarsa, ko a dukiyarsa, ko a makamantansu, sai ya ji rauni da gazawarsa sun bayyana, ya roƙi Ubangijinsa akan kowane irin yanayi ne ya sami kansa, shin yana kishingiɗe ne, ko a zaune, ko a tsaye, ya roƙi Allah ya yaye masa bala'in da ya faɗa masa, lokacin da Allah ya amsa masa addu'arsa, ya yaye masa wannan cutar, sai ya ƙaurace wa Allah, ya tsunduma cikin saɓa masa, ya manta falalar da Allah ya yi masa, kai ka ce babu wata cuta da ta same shi, kai ka ce bai taɓa roƙon Allah ya yaye masa ita ba, irin fa wannan hanya ce shaiɗan yake ƙawata wa kafirai abubuwan da suka aikata masu muni, da ɓatar da suka gabatar da aikata su)** [Yunus: 12]. Haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Ya Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), ka faɗa wa mushrikai cewa: wane ne wanda zai tseratar da ku daga firgici, gami da razanin da suke tudu, da koguna idan suka**

**fuskanto ku, kuka kuma fake da shi, kuna roƙonsa cikin ƙasƙantar da kai a zahiri da baɗini, kuna cewa: wallahi mun rantse da Allah idan har ka tseratar da mu daga barin wannan firgici za mu kasance cikin masu imani da iƙrari da falalar ka yi mana, za kuma mu gode maka kaman yanda ya kamata)** [al-An'ami: 63], lallai waɗannan ayoyin suna suranta mana halayen waɗanda suke ƙasƙantar wa Allah da kai da roƙon Allah a lokacin da suke cikin tsanani da damuwa, amma da zaran Allah yay aye masu wannan cutar sais u dawo akan abin da suke a kansa na munanan yanayi.

Lallai muna matuƙar buƙatar mu yi godiya akan ni'imomin Allah mai girma da buwaya a lokacin yalwa da wadata, mu kuma yi haƙuri a lokacin bala'i da jarrabawa, mu kuma dawwama wajen ambaton Allah mai girma da ɗauka a lokacin farin ciki da lokacin damuwa, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Wanda yake son ya yi farin ciki saboda Allah ya amsa masa addu'arsa a lokacin tsanani da baƙin ciki, to ya yawaita yin addu'a a lokacin yalwa da wadata)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Ka san da Allah a lokacin yalwa da wadata, zai san da kai a lokacin tsanani),** Sayyiduna Abuddarda'i (Allah ya ƙara yarda da shi) yana cewa: **Ka roƙi Allah a ranar farin cikinka, zai amsa maka a ranar damuwarka.**

**Ya Allah Ubangiji ka yaye wa kowane mutum da yake cikin damuwa, ka kuma azurta mu da yi maka godiya akan ni'imomi ba baiwarka.**